# SŨRATUL MASAD سُورَةُ المَسَدِ

Tana nũna hushin Allah ga maƙiyin Annabi. Kuma ita da sũrorin da suke bãyanta sunã nũna dogẽwar ƙiyayyar kãfirai ga addini bãyan ƙaurar Annabi, da dõgẽwar addini na gaskiya, kuma Allah zai tsare Musulmin ƙwarai daga dukan sharrin mãsu camfe-camfe da mãsu sanya dasĩsa a cikinsa.

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

*Da sũnan Allah, Mai rahama, Mai jin ƙai.*

*1.* Hannãye biyu na Abulahabi sun halaka, kuma yã halaka.

تَبَّتْ يَدَآ أَبِى لَهَبٍ وَتَبَّ ١

*2.* Dũkiyarsa ba ta tsare masa kõme ba, da abin da ya tãra.

مَآ أَغْنَىٰ عَنْهُ مَالُهُۥ وَمَا كَسَبَ ٢

*3.* Zã ya shiga wuta mai hũruwa.

سَيَصْلَىٰ نَارًا ذَاتَ لَهَبٍ ٣

*4.* Tãre da matarsa, mai ɗaukar itacen (wuta)[1].

وَٱمْرَأَتُهُۥ حَمَّالَةَ ٱلْحَطَبِ ٤

*5.* A cikin kyakkyãwan wuyanta akwai igiya ta kaba (Rãnar Kiyãma).

فِى جِيدِهَا حَبْلٌ مِّن مَّسَدٍۭ ٥

---

(1) Anã fassara shi da mai tsẽgumi, wãtau annamĩmanci; da Lãrabci anã ce wa mai annamĩmanci "mai ɗaukar itacen wuta".